











## TALLAFAWA DA KAYAYYAKIN KULA DA LAFIYA A NAJERIYA DA KULA DA MUTANE MARA LAFIYA DA SUKA RASA MAHALANSU DA WADANDA RIGINGIMU DA MAKAMAI YA RUTSA DA SU

Kungiyar agaji ta kasa da kasa ta ICRC da taimakon ma'aikatar kula da harkokin lafiya ta Najeriya tana kula da mutanen da suka rasa mahallansu da wadanda harsashi ya raunata su wadanda ke bukatar a yi masu tiyata cikin gaggawa. Haka nan mun horas da ma'aikatan lafiya da aka zabo daga wasu asibitoci, wadanan maikatan lafiya suna yin magani ga mutanen da rikici ya rutsa da su. Baya ga wannan ma kungiyar ICRC tana samar da kayan agaji na gaggawa da na tiyata da sauran kayan asibiti, a duk lokacin da ta samu turuwar mutanen da suka samu raunuka a dalilin fashewar bom ko wasu rigingimu.

Kungiyar agaji ta ICRC tana tallafawa cibiyoyin shan magani da asibitoci wadanda ke kula da mutanen da suka ji raunuka da wadanda suka rasa muhallansu ta hanyar samar masu da magunguna da kayayyaki don gyarawa ko daga martabar gine-ginen wadannan wurare.

## KAI DAUKI GA SAKAMAKON RIGINGIMU DA MAKAMAI KE SAMARWA

Kungiyar ICRC tana samarwa mutanen da suka rasa muhallansu kayayyakin da aka fi bukata a gida, kaman kwanonin girki da na tsafta, kayan kwanciya da kuma gidan sauro. Haka nan muna rarraba kayan samar da wurin kwana da abinci da sutura domin taimaka masu su samu jure rayuwa a yanayi na rasa muhallansu a lokacin da suka fi fuskantar karancin muhimman kayan rayuwa. Haka nan kungioyar ICRC tana samar da kayan noma na irin shuka da takin zamani ta yadda zasu iya ci gaba da noma. A wasu lokutan mukan taimaka masu su fara 'yan kananan sana'oi da zasu samu kudadden shiga.

Muna samar da wadannan taimakon ta hanyar hadin kan kungiyar agaji ta Red Cross ta Najeriya.

## BUNKASA HANYAR SAMAUN RUWAN SHA DA TSAFTAR MUHALLI

Kungiyar ICRC tana gyarawa ko daga darajar cibiyoyin samar da ruwan sha da tsaftace muhalli ga al'ummun da rigingimu ya rutsa da su a sansanoni da mutanen da suka rasa muhallansu. Duk ana wannan ne domin tabbatar da cewa mutane suna samun ruwan sha mai tsafta , muna aikin rarraba ruwan sha na gaggawa tare da bunkasa aikin samar da ruwan sha.

Kungiyar ICRC tana gina wuraren kwana na gaggawa domin mutanen da suka rasa muhallansu tare da samar da kayan muhalli na gaggawa ga al'ummun da aka fi fuskantar tashe-tashen hankula.

## AIKI TARE DA KUNGIYAR AGAJI TA RED CROSS TA NAJERIYA

Kungiyoyin agaji na Red Cross da ta ICRC suna aiki tare domin taimakawa mutanen da rigingimu da makamai ya rutsa da su, domin sake samun hulda da iyalansu da suka rabu da su. Ta hanyar tallafin kungiyar agaji ta ICRC, ma'aikatan sa kai na kungiyoyin agaji na Red Cross suna samar da taimakon gaggawa tare da kwashe mutanen da suka jikkata, da kawar da gawarwakin mutanen da suka mutu domin mika su ga hukumomi, domin tabbatar da cewa an adana bayanai don taimakawa mutanen da ke neman wadanda suka bace.

Kungiyar ICRC tana tallafawa kungiyoyin agaji na Red Cross wajen horas da jama'a gaba daya, musamman a kan tsarin sadarwa da kuma taimakon farkon na gaggawa a yankunan da suke cikin lungu inda babu ma'aikatan kula da lafiya.



R. Waudo/ICRC



M. Das/ICRC

## BUNKASA AIWATAR DA DOKOKIN KASA DA KASA NA KULA DA JIN KAN JAMA'A

Manufofin dokar kula da jinkan jama'a shine ta kare mutane daga dandana wahalhalu a lokacin rigingimu da makamai. A matsayinta na mai kula da wadannan dokoki, kungiyar agaji ta ICRC tana samar da kwararun lauyoyi domin tallafawa hukumomin Najeriya ta sanya tare da aiwatar da kudurorin dokar kula da jin kan jama'a a kasar. Muna taimaka horas da jami'an sojoji domin aiwatar da wadannan kudurori. Baya ga wannan jami'an rundunar 'yan sanda suna samun horaswa a kan dokokin kula da jin kan jama'a da kuma ka`idar aiwatar da dokokin kasa da kasa.


Tana aiki tare da kungiyar bunkasa tattali ta kasashen Afrika ta yamma watau (ECOWAS), kungiyar agaji ta ICRC tana bunkasa mutunta ko aiki da dokokin kula da jin kan jama'a a kasashen Afrika ta yamma, kuma muna aiki domin tabbatar da cewa kasashen da ke cikin kungiyar ECOWAS sun sanya hannu a kan muhimman kudurorin dokar kula da jin kan jama'a.

## BUNKASA JIN DADIN FURSUNONI DA AKE TSARE DA SU

Ta hanyar yarjejeniya da hukumomin Najeriya, wakilan kungiyar agaji ta ICRC suna kai ziyara ga fursunonin da ake tsare da su, domin duba hali da ma yanayin da ake tsare da su. Ana tattauna abubuwan da suka gani da hukumomin Najeriya, kuma ba'a bayyana su ga wani ko sauran jama'a. Idan bukata ta taso kungiyar agaji ta ICRC tana iya taimakawa domin bunkasa yanayin wuraren da ake tsare da su.

## MAIDO DA HULDA A TSAKANIN MUTANEN DA SUKA RABU DA IYALANSU

A duk lokacin da ya zama dole ga iyalai su bar gidajensu domin neman mafaka a wani wuri a matsayin gudun hijira, yakan faru 'yara sukan rabu da iyayensu. Mutanen da suka bar kasar da suke, sukan rasa hanyar sadarwa da iyalansu. Don haka kungiyar ICRC da kungiyoyin agaji na Red Cross ko Red Crescent suna aiki tare da sauran kungiyoyin agaji na Red Cross da Red Crescent domin taimakawa mutanen da suka rabu da iyalansu su gano tare da magana da 'yan uwansu, ta yadda zasu sake hadewa idan har akwai yiwuwar yin hakan




Kungiyar ICRC tana a Najeriya tun a shekarar 1988, kungiyar ICRC ta kuma yi aiki a kasar Najeriya a lokacin yakin basasa a 1967-1970.

ICRC Abuja
31 Pope John Paul II Street,
Maitama District, Abuja
P.M.B. 7654, Wuse III
T: +234 810 709 5551/2
abj_abuja@icrc.org

ICRC Gombe
T: +234 706 545 3493

ICRC Jos
1 Rest House Road, off D. B. Zang Road
GRA Jos
T: +234 813 353 6501
jos_jos@icrc.org

ICRC Kano
4 Maiyango Road
GRA Kano
T: + 234 64 91 27 33
kan_kano@icrc.org

ICRC Maiduguri
7 Bifam Road, off Circular Road (Damboa junct.)
GRA Maiduguri
T: + 234 810 713 9438
miu_maiduguri@icrc.org

ICRC Port Harcourt
46b Orogbum Crescent, Ayaminma Street
GRA II
T: + 234 84 46 02 70/1
poh_portharcourt@icrc.org

ICRC Yola
5 Girei Street, Jimeta
Yola
T: + 234 903 781 1043
T: + 234 903 781 1011
yol_yola@icrc.org

www.icrc.org
© ICRC, April 2015

ICRC

2015 0064/600 04.2015 20,000

Cover photo: A. Shaffa/ICRC



# ICRC A NAJERIYA

ICRC

A TAKAICE